# Shayarwa tana haramta dukkan abunda haihuwa take haramtawa

Daga Nana Aisha -Allah ya kara Mata yarda - daga Annabi - tsira da Amincin Allah su kara tabbata a gare shi ya : "shayarwa ta haramta duk abunda haihuwa take haramtawa"

[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim suka Rawaito shi]

Matan da aka haramta sabida dangantaka sune kamar Uwa, da yar uwa kwatankwacinta wacce aka shayar da ku tare, kamar Uwar da ta shayar da yar uwar da aka shayar tare dakai; don haka wani Hadisin yazo: "Abinda nasaba take haramtawa to shayarwa ma ta haramta" kuma wannan ya hadar da wajen Mata ne ko ta wajen Miji to dukkan wanda ya haramta na makusanci sabida Nasaba sabida ya aure ta kamar yar uwarsa da Innarsa da Gwaggwansa, to sun haramta a gare shi ya auri wadan nan idan ya kasance dangantakarsu ta hanyar shayarwa ya haramta ta auri Danta da Dan uwanta da Baffanta da Kawunta, duk wadan nan ya Haramta a gareta ta Aure su idan sun kasance tana da dangatakar shayarwa da su, kuma dai dai suke da makusantan ta wajen halaccin kallo ko kadaitaka da kuma tafiya, banda sauran hukunce hukunce, kamar gado ko da wajabcin ciyarwa da wasunsu sannan wannan haramcin da aka ambata na duba izuwa wanda aka shayar to cewa yan uwansa suma yan uwan wanda aka shayar da su ne tarebanda yayansa basu da alaka a tsakaninsu da wanda aka shayar, babu abinda yake na hukunci a tsakaninsu

https://sunnah.global/hadeeth/ha/show/4311